Idan Allah yana son Al-kairi ga Bawa sai yayi anfani da shi kafin Mutuwarsa

An karvo daga Umar Al-juma'i -Allah ya yarda da shi- cewa Manzon ALlah SAW ya ce: "Idan Allah yana son Al-kairi ga Bawa sai yayi anfani da shi kafin Mutuwarsa" sai wani daga cikin Mutane ya tambaye shi, ta yaya zai yi aiki da shi? sai ya ce: "Allah sai ya shirye shi zuwa aiki na gari kafin Mutuwarsa, sannan ya kavi rayuwarsa a kansa"
[Ingantacce ne] [Ahmad ne ya rawaito shi]

Lallai Allah idan yana nufin Al-kairi ga wani Bawa daga cikin Bayinsa sai ya datar da shi da aiki nagari kafin Mutuwarsa har ya samu ya Mutu kan wannan aikin, sai ya samu kyakkyawan Qarshe, sai ya shiga Al-janna

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/11203